# ZALUNCI DA DANNIYA: INA MAFITA?

Na

**Shaikh Ibraheem Zakzaky (H)**

Wallafar:
Cibiyar Wallafa Da Yaɗa Ayyukan Shaikh Zakzaky (H).
(Institute for Compilation and Publication of Shaikh Zakzaky's Works)

# ZALUNCI DA DANNIYA: INA MAFITA?

*Na*

## Shaikh Ibraheem Zakzaky (H)

**Wallafar:**
Cibiyar Wallafa Da Yaɗa Ayyukan Shaikh Zakzaky (H).
(Institute for Compilation and Publication of Shaikh Zakzaky's Works)

COPYRIGHT©

Institute for Compilation and Publication of Shaikh Zakzaky's Works.

Haqqin Mallaka (H): Cibiyar Wallafa da Yaɗa Ayyukan Shaikh Zakzaky (H).

## TUNTUƁA:

+234-70-68763600. +234-80-32-58-57-34. +234-80-37023343.


## MASANIYA:


LITTAFI: ZALUNCI DA DANNIYA:

MALLAKA: Shaikh Ibraheem Zakzaky (H)

NAKALTOWA: Ibrahim Musa (Edita).

JIGON BATU: Wa'azi da Farkarwa.

SHEKARA: 1439- Hij. 2018- Milad.

WALLAFA: Cibiyar Wallafa.

KANU: Fasali Biyar.

KALMOMI: Kalma 7,115.



ADIRESHI: Nigeria, West Africa.

TUNTUVA: 0706 8763 600 - 080-325-857-34.

Email; jawabanshaikhzakzaky@gmail.com



LITTAFI NA 18 A SILSILA

RAJAB: 1439.

GABATARWA:

Da Sunan Allah Mai Rahama Mai Jinƙai. Tsira da Aminci su ƙara Tabbata ga Fiyayyen Halittu, Annabin Rahama Muhammad (S) da Iyalan Gidansa Tsarkaka, da Sahabbansa Managarta.

Mai karatu, a wannan karon muna ɗauke ne da daɗaɗɗen jawabin da Shaikh Ibraheem Zakzaky (H) ya yi a wani taron 'yan boko, mai take Zalunci da danniya: Ina Mafita? Duk da cewa jawabin ya daɗe, amma kai ka ce a daidai wannan lokaci ya yi jawabin. Muna fata za a karanta jawabin cikin natsuwa da zurfafa tunani kan bayanan da Jagora (H) ya yi, domin lallai akwai abin la'akari mai girma.

Kamar kullum, aikin kwafo jawaban Jagora (H) daga kaset ɗin sauti zuwa rubutaccen littafi, aiki ne mai sarƙaƙiya da ke buƙatar Ihtiyaɗi, Lura da Taka-tsantsan. Mun yi iya ƙoƙarinmu wajan ganin mun kawo abubuwan da Jagora (H) ya faɗi a yadda suke ba tare da canzawa, ƙarawa ko rage komai ba, amma saboda ɗabi'ar magana da baki ta sha bamban da ɗabi'ar rubutacciyar magana, dole takan sa a wasu wurare a gyara wasu 'yan ƙananan abubuwa, kenan hakan ba zai rasa kurakurai da naƙasun fahimtar masu aikin ba. Abin sani dai shi ne, duk wani kuskure da aka gani a jawabin, to daga garemu ne masu aikin rubutawar, ba daga Jagora (H) ba, dan haka muna neman afuwa akan haka. Mun gode!

*Cibiyar Wallafa Da Yaɗa Ayyukan Shaikh Zakzaky (H)*
*TEL: 070-6876-3600. 080-3702-3343. 080-3258-5734.*

# GABATARWA:

‘Yan’uwa musulmi Assalamu alaikum warahmatullahi Ta’ala wa barakatuhu.
Maudu’in da aka ba ni da Ingilishi, an kira shi ‘Suppression and Oppression: The way out.’ Kuma lokacin da na ga maudu’in, na yi ɗan tunani daidai gwargwado, tunda ba yi na ba ne, ba ni ne na ba da maudu’in ba, an ba ni ne. Ban san mene ne su waɗanda suka ba ni maudu’in suke so haƙiƙani in faɗa ba. Ban san kuma ko duk abin da zan faɗa zai yi daidai da yadda suke zato ba, ala ayyi halin.

Ina da ko rauni ne ta nawa ɓangaren, sau da yawa in ina magana ina ƙoƙarin in ga maganar ta dace da maudu’in da aka ba ni. Komai daɗin magana in na ga ta fita maudu’in, sai in ga ta zama OP, wato ‘Off Point,’ ya fita abin da aka ce masa ya yi. Saboda haka zan so ya zama abin da zan yi ya dace da abin da ake tsammanin in faɗa.

Kuma ɗan daidai gwargwadon tunanin da na ba maudu’in, kasantuwar an sauya harshen da za a yi maganar da kuma sauyin waɗanda nake tsammanin za su saurari wannan lacca ɗin, sai har wala yau ya sake canza tunanina. Saboda da misali ’yan boko zan yi magana da su, kuma da Ingilishi, to ina jin daidai gwargwado dai zan faɗi abin day a dace da su, to amma Mai yiwuwa sauyin harshe zai sa akwai sauyin kalmomin da zan yi amfani da su da da Ingilishi ne. Kuma kasantuwar waɗanda za su saurare ni, ba waɗanda nake tsammani ne ba, har wala yau dole abin da muhadarar ta ƙunsa ya zama ta sake. Saboda haka har wala yau na sake shiga wani irin ƙunci na cewa ban san in na yi magana za ta dace da abin da ake tsammani daga gare ni ba.

Da yake maudu’in da Ingilishi aka bayar, ‘oppression’ dai yana nufin zalunci ne, wanda galiba ake ganin wanda ke da iko yake yi a kan waɗanda yake da iko a kansu; musamman ma dai rashin adalci a wajen hukunci da kuma rashin adalci a wajen rabon haƙƙoƙi. Wanda duk ya riƙe haƙƙoƙin wasu ya ƙi y aba su, ko da haƙƙoƙin nan dukiyoyi ne nasu ko mene ne, za a iya cewa ya zalunce su. Haka nan kuma idan

wajen hukunci ne, ya zama ga abin da yake daidai, ya kauce daga abin da yake daidai, za a iya cewa ya zalunce su.

'Suppression' kuwa wani yunƙuri ne na a hana wani abu tasowa, wato wani abu ne yake yunƙurowa sai a matse shi; kamar wata murya tana neman ta ɗago, sai a yi ƙoƙarin a ga an rufe muryar ma ba a ji ta ba. Kamar waɗansu mutane suna ƙoƙarin su kafa wata ƙungiya, sai a yi ƙoƙarin a ga an tarwatsa su, a kuma ga cewa lalle ba su kafa wannan ƙungiya ɗin ba. Ko za su kafa wata jarida don ta faɗi wani ra'ayi, sai a yi ƙoƙari a ga an kawar da wannan, ko da ƙarfi ko ta halin yaya, ko ta hanyar yaɗa farfaganda. Ko kuma wata murya wadda ake neman a ayyana wacce ta saɓa wa wadda shi mai danniya yake a kai, shi kuma yana ƙoƙarin ya ga cewa wannan muryar ba ta ɗago ba samsam. Muna iya cewa duk wannan abu guda ne. Waɗanda suka gabata da jawabi sun fassara abin da Hausa, suka ce zalunci da danniya. Danniya shi ne 'suppression' ɗin, kamar a danne wani abu mai neman ya ɗago.

## MA'ANAR MAUDU'IN:

Wannan maudu'i ne da ba a ce a ina ne ba. Amma na ji wani ya ce a ƙasar nan. Amma ni an ce min zalunci da danniya: Ina mafita? Kamar ka ce su waɗanda suka ba da maudu'in nan suna tunanin muna wani nau'i ne na zama cikin zalunci da danniya ɗin, kamar kuma ana neman ta ina za a fita daga wannan danniya ɗin. In haka nan ne abin da ya hau kaina shi ne in fassara ma'anar zalunci da danniya ɗin daidai gwargwado, sa'ilin nan in kawo yadda za a yi a fita.

Na farko wannan maudu'i ne da za a iya sa shi a kowane. Wato wannan maudu'i da aka ba ni kamar yadda yake 'oppression and suppression: The way out' yana iya zama maudu'i wanda 'yan Kwaminis za su tattauna a kai. Wato ko da 'yan Kwaminis aka ce musu ga wannan maudu'in ko tattauna a kai, ba za su rasa ta cewa ba. Ta yiwu su ce an matse haƙƙoƙin talakawa, masu hannu da shuni sun riƙe komai da sauransu. Har wala yau masana halayyar zaman ɗan'adam ana iya ba su su tattauna wannan maudu'i. Masana 'sociology' kenan. Su ma yana

iya zama maudu'i a wurin su. Su ce tarihi ya nuna in ɗan'adam ya samu muhalli da iko sau da yawa yakan yi kama-karya. Da zaran ya ji wata murya tana neman ta ɗago tana kishiyantar abin da yake yi, yakan ƙoƙari ya danne wannan muryar. Kuma har wala yau wannan maudu'i ma kila ko a coci ana iya kai shi a tattauna shi. Ban san dai abin da su Fasto za su ce ba, amma na san maudu'i ne da a ilmance ana iya kai shi kowane muhalli a tattauna shi. Amma tunda yake wannan dandali namu na addinin Musulunci ne, to ko ba a gaya wa kowa ba, ana son mu kalle shi ne a musulunce.

Har wala yau kuma wannan wani ɓagare ne na 'Seminar' na kwana uku wanda aka ƙaddamar da wasu laccoci, ya fara jiya Juma'a, zai kuma ƙare gobe Lahadi. Saboda haka dukkan abin da za a gabatar yana ƙarƙashin wani maudu'i na taron gaba ɗaya na kwana uku wanda aka kira 'Leadership crises in Nigeria', wato kamar matsalar shugabanci a Nijeriya. Ta haka nan za mu iya cewa ashe wannan maudu'i namu, Zalunci da danniya; ina mafita? Za mu gan shi ne a wannan faffaɗan maudu'i na matsalar shugabanci a Nijeriya. Aƙalla haka nake tsammanin waɗanda suka ba da maudu'in suke nema.

## ZALUNCI DA DANNIYA:

To, na farko zalunci. Zalunci kamar yadda na riga na faɗi ma'anarsa na lugga shi ne mutum ya ci haƙƙin wani. Haƙƙin nan na iya zama kayan wani, ko kuma yana iya zama wani haƙƙi ba na kaya ba, ko da na damar ya faɗi ra'ayinsa ne ko kuma haƙƙin ya san wani abu. To in ya zamana an hana shi wannan haƙƙin, to za mu iya cewa an zalunce shi.

Zalunci yana iya zama har wala yau ta fuskar yin shisshigi a kan haƙƙin wani. Wato ko da ba a danne shi ba, an kutsa masa, an tauye masa ko yaya ne. Saboda haka muna iya cewa kishiyan zalunci shi ne adalci. Adalci yana iya zama daidaita mutane da kuma daidaita su a wajen rabo. Alal misali da za a ce mun haɗu za a raba wani abu da yake duk namu ne, to a raba shi daidai wa daida zai zama adalci. Kodayake wani lokaci adalci ba ya nufin daidaito. Alal misali inda za mu ci abinci

ne aka ce to kowane mutum a ba shi daidai yawan kada ya fi na kowa, to za mu ga cewa mai babban ciki an ƙware shi, kuma an yi wasa da yaro. Kamar ga yaro ɗan ƙarami sai a kifa masa ƙaton malmala. Mai babban ciki kuma zai iya cinye wannan malmala ɗin, shi kuma ƙarami zai tsakura ne ya zubar da sauran, to ba zai zama an yi adalci ba. Adalci ba lalai yana nufin daidaito ba ne.

Har wala yau muna iya cewa, shisshigi shi ma kishiyan adalci ne. Wato kamar mutum ya kutsa cikin abin da yake haƙƙin wani ne. Na wani ne ba nasa ba. Saboda haka za mu ga a isɗilahin Alƙur'ani wannan kalma 'Zulm' ta zo a wurare da yawan gaske a Alƙur'ani. Kai ka ce Kalmar 'Zulm' ɗin nan, zalunci wani abu ne wanda yake a wurin Allah Ta'ala yana da muhimmanci, tunda a wurare daban-daban a Alƙur'ani za ka ji kalmar Zulm ta ɓullo, ko da sunan Zulm ɗin ko da sunan su azzalumai ɗin, ko wane ya fi zalunci, "Waman azlamu mimman" kaza da kaza. Za ka ga a wurare da dama Allah ya ce wa ya fi zalunci fiye da wanda ya yi kaza, ya yi kaza. Zan dawo kan wannan in na zo kan nau'o'in zalunci.

Sannan kuma za ka ga wurare inda ya ambaci zulm ɗin da sunan zaluncin. Kamar inda yake cewa "Innas shirka lazulmun azim." Kuma akwai hadisi Kudsi inda Allah (T) yake cewa "Ya ku bayina na haramta wa kaina zalunci, kuma na ajiye zalunci ya zama a tsakanin ku haram. Saboda haka kar ku zalunci junanku." To, 'Zulm', 'Zulm', ga shi nan birjik a cikin Alƙur'ani, kuma birjik a cikin hadisin Manzo.

Kazalika kuma abin da ke kishiyantar zulm ɗin nan, su ma za ka gan su kalmomi ne da suka zo a wurare daban-daban a Alƙur'ani. Su ne 'Adal', adalci ke nan. Shi ma za ka gan shi a wurare daban-daban a Alƙur'ani, inda Allah (T) ke umurni da 'Kisɗi' ko 'Adal'; duk dai abu guda ne. Kisɗ kamar ana nufin a yi abu daidai, ya yi 'balance' kenan. Adal shi ma kazalika, abin da yake nufi kenan. Kamar inda Allah (T) yake cewa 'Innallaha yuhibbul muƙsiɗin." da kuma "Wala ta'atadu innallah la yuhibbul mu'utadin." Wato za ka ga yana ta kawo Adal, adal

a wurare daban-daban. Yana umurni da yin 'ƙisɗ' da hani ga barin zalunci.

Har wala yau ɗaya kishiyar na adalci, wani ma'anar na zalunci shi ne shisshigi. Shi ma kishiya ne na adal. Muna iya cewa zalunci ana iya yin sa ta hanyar shisshigi. Shi ma za ka ga ana ta nuna 'bagyi', 'bagyi' a wurare da dama a cikin Alƙur'ani. Kada mutum ya yi bagyi, wato kada mutum ya kutsa cikin haƙƙin wani.

To, a isɗilahin Alƙur'ani muna iya cewa 'zulm' ɗin nan ya zo a wurare daban-daban, kuma an bayyana mana nau'i daban-daban na zalunci. Na san daidai gwargwado ba zan iya faifayewa da kowane irin nau'in zalunci ba, amma daidai gwargwado zan yi ɗan ƙoƙari in tunatar da mu ta inda ake yin zalunci da kuma nau'o'insa, ko da ban faɗi kowanne ba, amma na faɗi wasu.

Ɗaya daga cikin zalunci, wala'alla ma shi ya fi kowane nau'in zalunci girma shi ne zaluntar kai. Mutum ya zalunci kansa da kansa. Sau da yawa in muna maganar zalunci, nan da nan abin da ke faɗowa a ƙwaƙwalwar mutum shi ne mai hukunci wanda ya danne haƙƙin waɗanda suke ƙarƙashinsa. Mai yiwuwa nan da nan abin da zai faɗo tunanin mutum kenan. Kila ma waɗanda suka ba ni maudu'in abin da suke tunani kenan. Suna tunanin masu hukunci a ƙasar nan suna danne haƙƙoƙin waɗanda suke hukunci a kansu.

To, akwai wani zaluncin da ya fi wannan girma, wanda in an shafa cikin mu ɗaiɗai ne, kila ma duk cikan mu azzalumai ne. Saboda zaluntar kai shi ne ya fi kowanne girma a zalunci. Wannan ba wani ne ya zalunce ka ba, kai ne ka zalunci kanka. Wannan yana iya bayyana ta hanyoyi da daman gaske wanda yake, mutum shi ne ya zalunci kansa. Bari in ba ku ɗan misali inda nake cewa duk cikan mu azzalumai ne ta wannan fuskaci. Sau da yawa akwai wani abu wanda za ka ga cewa yana da kyau ka yi, amma sai ya zama ba ka yin ba; wannan abin kuwa ko da taimakon wani gajiyayye ne ko wani ɗan'uwanka. Kana son ka taimake shi, amma kuma kana aunawa, kai ma kana buƙata, shi ke nan sai ka yi

mirsisi da idonka, ba ka yi taimakon ba. To, ka ga za ka iya, amma ba ka yi ba. A nan ka ƙwari kanka ne. Shi ma nau'i ne na zalunci. Ina ba ku misali ne, na cewa mutum, babban zaluncin da zai yi shi ne ya zalunci kansa.

Wata fuska ta zaluntar kai, wanda yake sananne ne shi ma Allah ya yi magana kan wannan a cikin Alƙur'ani, shi ne inda mutum zai ga ga gaskiya, ya kuma san ita ce, amma sai ya danne ta. Wannan ɗabi'a ce ta mutum, sai wanda Allah Ta'ala ya tsamar. Allah Ta'ala a bisa halittar da ya yi mana, ya riga ya halicci kowane mutum ya sa masa wani haske a zuciyarsa. Shi wannan haske halittacce ne tare da zuciya. Kuma ba ya rabuwa da zuciyar mutum. Hasken nan yana taimaka wa mutum ya gane gaskiya in an faɗe ta. Duk lokacin da wani mai Magana ya gaya maka gaskiya; in dai gaskiya ya faɗi, to wannan hasken zai ɗan motsa. Za ka ji shi a ranka, amma ban ce lalai za ka faɗa ba. A ranka za ka gane wannan abin da yake faɗa daidai ne. Ban san ko da Turanci za a iya kiran sa 'conscience' ba, wanda yake a zuciyar mutum yake. Da an faɗa mutum zai ji shi haka nan yake kawai.

Amma fakam da yawa mutane in an faɗa musu, suka ji, kuma a zuciyarsu suka gane haka ne, sai su yi mirsisi da idanunsu su ce ba haka ba ne da bakinsu. Har ma wala'alla su sa hannu. Amma suna faɗa ne da zuciyarsu, saboda zuciyarsu tana gaya musu wannan abin da kuke yi ba daidai ba ne. Wannan wani nau'i ne na butulci, shi kuma wani nau'i ne na rashin adalci. Shigen irin wannan ne Allah Ta'ala yake cewa, "Innal insana lirabbihi lakanud. Wa innahu ala zhalika lashahid." Wato mutum mai tsananin butulci ne ga Ubangijinsa, kuma shi mai shaida ne kan wannan. Wato ya sani a ransa, amma kuma sai ya ce ba haka ba ne.

Wani abu sananne ne wanda Allah ya riga ya halicci mutum da shi, shi ne sanin Allah. Sanin Allah halittacce ne a zukatan mutane. Allah da ya halicci mutum, ya riga ya sa masa sanin Allah a zuciyarsa. Saboda haka ba wani mutum da bai san da akwai Allah ba. Ko da Bamaguje ne ko arnen kan dutse ne ya san akwai Allah. Wannan ko ba a koya masa ba. Ko da ma tana iya yiwuwa wani jariri ne ya ɓace daga gun iyayensa,

ya yi daji, bai san kowa ba, wata damisa ta rene shi, ya riƙa shan nonon damisa, ya girma a daji, shi bai san kowa ba, cikin dabbobi ya girma, to zai kasance ya san Allah. Wani ilimi ne da ba ka buƙatar a koya maka saboda halittacce ne.

To, amma wannan bai isa ya shiryar da mutum ba, koda yake ya san da wannan. Sai idan aka zo masa da bayani ta waje, bayanin Allah Ta'ala, shi ya halicci sama da ƙasa, za ka ga a ransa ya sani, ya gane haka nan. To, amma sau da yawa saboda tsananin zalunci ga kai, ɗan'adam sai ka ga ya yi mirsisi da idanunsa ya bututtuke ya ce shi ba haka ba ne. Kuma da za a tambaye ka a ce wane abu ne ya fi yi wa ɗan'adam wahala? Wane abu ne ya fi wa mutum wuya da ya yi? Sai ka ce amsa shi ne, ya yarda cewa Allah ɗaya ne. Ta yiwu ku sha mamaki, ya yarda Allah ɗaya ne? To, kuma haka ne. Ɗan'adam wannan yana yi masa wuyan gaske, ya yarda da Allah ɗaya ne.

Muna kuma iya cewa wannan shi ne babban zaluncin da yake yi wa kansa. A ransa ya san cewa shi ɗaya ne, amma ya yarda zahiran, a sarari ya ce hakan ne Allah ɗaya ne, to yana yi masa wahala. Duk yadda za ka yi da shi, ba ya ji, sai ya gwama Allah da wani abu, to sannan sai ka ga yana farin ciki. Koda yake ya san ba haka ba ne, amma za ka ga ya yi masa daidai. Abin mamaki da ɗan'adam ke nan. In dai ya gwama Allah da wani, to shi kenan sai ka ga yana farin ciki. Amma da zaran an ce Allah ɗaya, sai ka ga yana masa wahalar ya yarda.

Kuma wannan shi ne sanadiyyar da ya zama da yawan al'umma suka ɓace a kan zaluntar kawukansu. Kamar yadda Allah (T) yake cewa dangane da waɗanda ya karɓi rayukansu, "Innallazina tatawaffahumul mala'ikatu zalimi amfusihim.." Wato waɗanda Mala'iku suka ɗauki rayukansu suna masu zaluntar kawukansu. Wanda yake babban zalunci shi ne mutum bayan sun yi karo da zuciyarsa, ya danne gaskiyar da ke cikin zuciyarsa, ya yi abin da yake so, saɓanin abin da yake ya san cewa shi ne gaskiya. Kamar wannan aya da nake ce muku, "Innal insana li rabbihi lakanud. Wa innahu ala zhalika lashahid."

An ce wani ya taɓa zuwa wajen Manzo ya ce da shi, ka zo neman fatawa ne? Sai ya ce da shi eh. Sai ya ce, to binciki zuciyarka. Ya ce masa, "laifi shi ne abin da ka ji yana maka yawo a rai, ka kuma ƙi mutane su gani, ko da ko Malamai sun yi maka fatawa." Wannan ya nuna akwai wani ilimi zaunanne a zukatan mutane, komai jahilcin mutum Allah ya saka masa wannan ilimin. Ta wannan ne ya zama komai maluntar Malam, in ya faɗi wata magana ba daidai ba, komai jahilcin jahili, sai ya ji maganar ta zama bambaraƙwai. Sai ka ga jahili ya yi shiru, ya dubi Malamin haka nan. Shi bai yi karatu ba, amma wani abu zai sa masa tunanin cewa abin da Malamin nan ya faɗi fa ba haka ba ne. Wannan yana taimaka mana ga gane gaskiya. Kamar yadda Manzo yake cewa ko da duk duniya ta yi maka fatawa, in dai a zuciyarka ka ji ranka ya yi maka haka, da Kyar ba haka ɗin ba ne. Don ita gaskiya, Allah ya riga ya saka mana ita a rai.

Muna iya cewa ɗan'adam sau da yawa duk tsawon rayuwarsa yana faɗa da wannan abin ne. Sai ya yarda da wannan gaskiyar da ke cikin zuciyarsa, ya fi ƙarfin wannan, zai iya karɓan gaskiyar da ta zo ta waje. Muna iya cewa duk lokacin da Manzanni suka zo suka kawo saƙo, to mutane suna ganewa, ba ba sa ganewa ba ne. Ko Fir'auna da Musa ya zo masa ya ce da shi Allah ya aiko shi, ya tsaya a gabansa a fadarsa, ya san da gaske ne. Yana faɗa masa, ya gane da gaske ne. Amma kuma a nan Fir'auna ya yi faɗa da ransa ne, yanzu shi zai iya yarda ya ce wannan abin gaskiya ne, koda yake ya san gaskiya ne? In ya yi haka nan yaya matsayin da ya faɗi da? Yanzun zai faɗa masu gaskiya cewa da can shi maƙaryaci ne a da'awarsa cewa 'Ana rabbukumul a'ala'? lokacin da ya gaya wa mutanensa cewa shi ne Ubangijinsu Maɗaukaki. Ko kuwa yaya?

In ya ce eh, tun da na san Allah shi ne Mahaliccin sama da ƙasa, shi ya yi kowa da komai, kuma shi ya cancanta a bi, saboda haka jama'a, mu zo a bi Musa." Sauran jama'a za su ce oho ashe da ma da kake cewa kai ne Ubangiji Maɗaukaki, ashe ƙarya kake yi?" Saboda haka sai Fir'auna ya yi mirsisi ya ce, "faman rabbukuma ya Musa?" Waye Ubangijin naku? Musa ya ce wanda ya ba kowane abu halittar sa, ya

shiryar da shi.” Ya ce, to waɗanda suka wuce fa?” A wani wuri yake cewa “wane ne Ubangijin naku?” Ya ce, “Ubangijin sammai da ƙassai da ...” Sai ya dubi fadawa ya ce Manzon da aka aiko muku fa Majnuni ne. Ya kuma ce masa “La’inittakhazta ilahan gairi, la aj’alannaka minal masjunin.” Wato in ka riƙi wani Ubangiji ba ni ba, in ji Fir’auna, to zan sa ka a cikin Fursunoni. Wannan Fir’auna yana ta faɗa da kansa ne. Don haka ne ma ya yi ƙoƙari ya kawo masu sihiri, suka ƙwama da Musa. Su masu sihiri, da gani, suka gane. Su sai suka fi ƙarfin zukatansu. Ba su yi kwaɗayin abin da Fir’auna zai ba su a fada ba. Sai suka ce wannan na Allah ne. Da gani sun san ba sihiri ba ne. Sai suka bi. Amma Fir’auna sai ya sake canzawa ya ce, to shi ke nan wannan shiri ne, da ma can wannan shi ne Malaminku da yake koya muku sihiri don a zo a ruɗi mutane a ce musu…Amma Fir’auna ya sani duk ba haka ba ne. Kar ku ce wai Fir’auna ya jahilci abin ne. Ina ba ku misali ne, kar in cika ku da bayanai dangane da wannan.

Abin da nake ƙoƙarin na ce shi ne, wannan nau’i ne na zalunci da kowannen mu, sai ya fi ƙarfin wannan zaluncin kafin ya kuɓuta. Wato zaluntar kai, wanda yake mutum yake iya ganin gaskiya, sa’ilin nan kuma ya ƙi bi.

Akwai wani wuri da Allah Ta’ala yake ba da misalin bayinsa kamar siffa uku. Ya ce, “Faminhum zalimun linafsihi, wa minhum muƙtasiɗ, wa minhun sabiƙun bilkhairati bi iznihi.” Wanda masu fassara sun kawo saɓani a kan su wane ne ake nufi. Wasu suka ce duk cikan su muminai ne, su uku ɗin nan. Ɗaya sabiƙun bilkhairati, shi ne ya gane gaskiya, ya kuma yi iyan ƙurewa don abin da zai iya yi. Ɗaya kuma muƙtasiɗ mai taƙaitawa, zai iya yin fiye da abin da yake yi, amma kuma sai ya yi ɗan kaɗan. Zalimun linafsihi kuma sai ya yi ɗan kaɗan ƙwarai ƙwarai da gaske.

Wasu kuma suka ce zalimun linafsihi shi ne wanda ya ƙi ya yi, wato ya butulce ke nan. Muƙtasiɗ kuma shi ne wanda ya taƙaita, zai iya yin fiye da haka. Sabiƙun bil khairat kuma shi ya wuce. To shi ne wanda ya yi adalci, ya iya yin daidai gwargwadon abin da yake iyawa. To na

faɗa mana wani nau'i ne na zalunci don kowannen mu ya shafa ya gani shi ma ta wannan ɓangaren azzalumi ne, kuma ya kamata ya yi wa kansa adalci. Koda yake adalci irin wannan na da wahalar gaske na ainihin ka ga gaskiya, gaskiya, ka san ita ce, ka yi hukunci da ita, ka yi aiki da ita.

## INDA ƊAN'ADAM YAKE GWAMA WANI TARE DA ALLAH

To sai kuma abin da ya biyo bayan wannan. Na ma faɗi wani abu a kansa a baya. Shi ne inda ɗan'adam yake gwama wani tare da Allah. Wanda kuma shi shaida ne a kan cewa lalle Allah ba shi da abokin tarayya. In ka tambayi ɗan'adam wane ne ya halicci sama da ƙasa, kowane ka tambaya, zai ce maka Allah. In ka ce wa mutane wane ne ya halicce ku? Kowannensu zai ce maka Allah. Kuma in ka tambaye su, to wane ne ke azurta ku? Yake saukar da ruwa daga sama, wane ne ya samar da iskar da kuke shaƙa da sauransu? Duk za su ce maka Allah. Amma a lokaci guda in aka zo aka ce, to wane ne ke nan ya fi cancanta da a bauta masa? To, a nan fa babban zaluncin zai zo, wanda Allah (T) yake cewa, "Innas shirka lazulmun azim." A nan fa ɗan'adam ya sani, ba bai sani ba; amma yana masa wahala ya zama bai gwama Allah tare da wani ba.

Na faɗi wannan ɗazun, koda yake na shigar da shi, in aba da misali da zaluncin da mutum yake wa kansa. To yanzu na fito da shi ne a zaluncin ƙashin kansa, wanda muna iya cewa shi ne tushen kowane irin zalunci, gwama Allah da waninsa. Wanda yake kuma kowa shaida ne a kan cewa Allah ba shi da tsara, Allah ba shi da sa'a, Allah ba shi da abokin tarayya. Ba shi ma da waziri, ba shi da 'Assistant', ba shi da 'Deputy', ba shi da Minista. Allah Ta'ala abin da ya ga dama yake yi, shi ne mai tasarrufi a abin da ya so, yadda ya ga dama. Wannan kuma sanin kowa ne a bisa ilimin da Allah ya sanasshe shi, sai dai ilimin na waje, na saƙon da aka aiko ya sanar da mutum, ya ƙara wa mutum yaƙini. Amma sanin wannan, kamar wani abu ne zaunanne a zuciya.

Wannan zaluncin na gwama Allah da wani, sau da yawa mutane in aka ce musu gunki, sassaƙaƙƙen gunki, wanda akan sassaƙa da katako

ko aka kankaro shi daga dutse, ko a narka ƙarfe a yi da shi, ko a kwaɓa ƙasa a jajjaɓa shi, a yi masa siffa irin ta halittar mutum ko wata dabba, sannan sai a zo a bauta masa, a ce wai shi Ubangiji ne. To wannan sukan fahimta. Da zaran an ce wannan zalunci ne babba, kowanne sai ka ga ya ce lalle bai kamata ba, Allah Ta'ala ya halicce ka, ka bauta ma waninsa.

Ta yiwu faɗin nan da nake yi cewa in ka tambayi mutum, wane abu ne ya fi wahala ga mutum ya karɓa? Nake cewa ya yarda Allah ɗaya ne, to za ka gane wannan, duk lokacin da aka da mutum ya zo ya bi dokar Allah. Allah Ta'ala yana cewa a littafinsa "wa iza zukirallahu wahadahus ma'azzat ƙulubullazina la yu'uminuna bil akhira. Wa iza zukirallazina min dunihi izahum yastabshirun." Ma'ana, in an ambaci Allah shi kaɗai, sai ka ga zukatan waɗanda ba su imani da lahira ba duk sai su ƙwansare, ka ga mutum ya ɓata rai; wai ka ce Allah ɗaya ne. Amma da zaran ka ɗan gwama da wani, sai ka ga kawai kowanne ya yi ɓasha da baki, ya yi daidai. Wannan wani abu ne har yanzu. Kar ka ɗauka ga masu bautar gumaka ne, har yanzu.

Inda za ka gane wannan, da za ka ce, ba za a bi dokar kowa ba, sai Allah; da ka ta da hankula. Za ka ji an ce to wanda muka gada kuma fa? Wanda muka gada tun iyaye da kakanni fa? Shi kuma wanda bature ya zo da shi fa? Yanzu wannan ci gaban zamanin fa? Amma da za ka ce, ko Allah ɗin ma ai ya yarda cewa .., sai ka ga kowa ɓasha, ka ji gaskiya. Wato ko Allah ma ya yarda a ɗan aje dokarsa ma a bi ma wani abu.

Wannan a bisa gaskiya ba ƙaramin zalunci ba ne. In da za a tambayi mutane wa ya halicce ku? Za su ce Allah. Har wani ya taimaka masa a wajen halittar ku? Za su ce a'a. Saboda haka wane ya cancanci a bauta masa? Dokokin wa ya kamata a bi? A nan za a ga cewa Allah ne ya kamata a bi. (A AUDIO DIN AKWAI ABIN DA YA YANKE A DAIDAI NAN GUN).

Sannan sauran mutane, iyayenka ne, matanka ne, maƙwabtanka ne, mutanen garinku ne da sauransu, duk suna da haƙƙi a kanka. Haƙƙin da ya fi kowanne girma a kanka, ya kamata ya zama na wa? Na Allah

Ta'ala. To, ashe in ka ci da haƙƙin Allah, to lallai ka ƙwari Allah ɗin kenan. Koda yake sakamakon zaluncin kullum yakan koma wa azzalumi ne, wanda daga ƙarshe za mu ga in ma ka zalunci Allah, to sai dai mu ce ka zalunci kanka ne kawai, don sakamakon zaluncinka zai koma ƙarshe zuwa gare ka. Ta wannan za mu iya cewa ba a yi wa Allah adalci ba in aka gwama shi da wani. Ko aka gwama wasu dokokinsa da na wani, ko aka ƙi bin dokarsa, aka ɗauko wani abu daban aka bi. Shi ma nau'i ne na zalunci.

To, da yake adalci rabon haƙƙoƙi ne daidai wa daida; na ma riga na faɗi waɗanda suke haƙƙoƙi ne a kanka, muna iya cewa ka ga haƙƙin kanka da haƙƙin Ubangijinka, sai kuma haƙƙin wani mutum ɗan'uwanka a kanka da kuma haƙƙin wasu halitta ma, dabbobi da ma haƙƙin muhalli. Ko kun san muhalli ma yana da haƙƙi? Ba ku ga ɗan'adam, sakamakon zaluncin da ya yi wa muhalli, an sami abubuwa da dama suna ta aukuwa a ƙasa, sakamakon ɗan'adam yana ta cutar muhalli ta wajen gurɓata shi. Sai ya zama ya haifar da abubuwa da daman gaske. To, shi ma wani nau'i ne na zalunci.

To, wala'alla zaluncin da ya fi ɗauke hankulan mutane, wanda kuma yake kila shi ne masu maudu'in suka ba ni suke so in yi magana a kai, kila su ce duk na cika su da surutu kan wasu nau'o'in zalunci, su kawai zaluncin shuwagabanni kan waɗanda suke bi. To, ina tsammanin ni zan ba ku mamaki, a nan zan gaya muku cewa da shuwagabannin da mabiyan duk azzalumai ne! Domin Manzon Allah (S) yana cewa ka taimaki ɗan'uwanka azzalumi ko mazlumi. Sai Sahabban Manzo suka ce, "Ah, Ya Rasulullah wannan mazlumi, wato an zalunce shi, za mu iya fahimtar mu taimake shi, to ya za mu iya taimakon azzalumi kuma?" Sai Manzon Allah ya ce, taimakonka ga azzalumi shi ne ka taimake shi ga barin yin zaluncin, ka hana shi yin zaluncin. Idan ya zamana kai ma ka taimaki azzalumi ya yi zalunci, to me ka yi ke nan? Kai ma ka yi zaluncin ke nan!

A nan ko an zalunce ka akwai wani taimakon da za ka yi na hana azzalumi yin zalunci. In na lura da maudu'in nan na shugabanci, koda

yake ba shi aka ba ni ba, amma shi maudu'in zaluncin yana ƙarƙashin wannan ne, batun matsalar shugabanci a ƙasar nan, muna iya cewa ƙasar nan ta gamu da irin waɗannan nau'o'i na zalunci a marhalolin da ta shiga daban-daban. Na farko gab da zuwan Bature ta gamu da wani irin nau'i na zalunci daga Sarakai waɗanda suke taƙama da jinin Shehu Usmanu Ɗan Fodiyo, ko jinin waɗanda Shehu ya ba tuta, amma suke aiki irin na Kakansu a aiki Bawo Ɗan Bayajidda, wanda ya kashe macijiya a rijiyar Kusugu. Wato a addinance sun gaji Ɗan Fodiyo da waɗanda Ɗan Fodiyo ya ba tuta, amma a aikace Bamaguje ne Kakansu.

Sai ya zama a wannan lokacin an samu wani irin nau'in zalunci, wanda ya gwama Musulunci da Maguzanci, wanda ya mai da Sarakunan Hausa a wannan lokacin suna Musulmi, amma suna sarauta da salon sarauta cakuɗe da Maguzanci da kuma son ransu. Saboda haka a wannan lokacin, sai ya zama an samu wani irin nau'in danniya, aka ci da haƙƙin waɗanda ake wa shugabanci, aka raba littafi da shugabanci. Ya zama da can Shuwagabanni Malamai ne, sai ya zama an canza, yanzu ba Malamai ne ke shugabanci ba. Da can alamin shugabanci shi ne ilimi da tsoron Allah, saboda haka ma ba mamaki a ga Amir a kasuwa yana duba mudu, ya ga ko wa ya tanƙware? Yana duba nono ya ga ko an zuba masa ruwa. Yana zuwa sassa daban-daban. Da dare ma yakan zaga gari ya ga ko masu gadi suna gadi, kowa yana bakin aikinsa.

To, amma daga baya da abin ya tashi daga ilimi da tsoron Allah, ba su ne alamin shugabanci ba, sai ya zama dole shugabanni su sami wani alami. Sai suka sami wani alami na ba da tsoro. Wala'alla daga nan ne ma sai suka yi wa rawaninsu ƙaho, domin su zama kamar waɗansu dodanni. Sai kuma su ɗauki rawanin nasu su sauko da shi ƙasa, su ɗauki wani sashe su rufe har hancinsu, sai idanun za ka gani zuru-zuru. Saboda haka tunda ga Sarki ba shi da karatu, in ya yi magana za a sha mamaki, sai aka ce shi ba ma ya magana. Sai kawai ya yi muzurai ga ƙahonsa, ga idanunsa. (AN SAMU KATSEWAR JAWABIN A NAN MA).

Mu mutane ne da muka kasa samun ta'arifi, wato ba mu da 'defination.' Sunanmu mene? In ka ce mana 'yan Nijeriya, sai mu ce, to

ai kuma sunanmu musulmi. Bai fiye mana haka ba? To, wanne ne mu? Sai ka gan mu cikin wani irin ɗimuwa. Ya kamata mu ɗauki ɗaya mu ɗora kan ɗaya, imma wannan, wa imma wannan. Shi ya sa aka rinƙa samun matsala dangane da al'amarin shugabanci.
Mene ne adalci a al'amarin shugabanci? Adalci shi ne 'yan ƙasa duk cikansu su kasance duk bai ɗaya ba tare da la'akari da bambancin ƙabilarsu da addininsu ba? Kuma kowane ɗan ƙasa yana iya zama Shugaba kuma a bi shi? Idan aka ce min eh a rubuce haka ya kamata a tsarin mulki, mun yi ittifaƙi haka nan ne misali. To, sai kuma a zo a aikace, sai ka ga ba haka nan ba ne. Mutane ba su gamsu ba.

Kuma sau da yawa ko an zo kaɗa ƙuri'a ne, mutane suna tunanin wannan addininmu ɗaya, wannan ɓangarenmu ɗaya. Ko ba su tunanin haka nan? Sai kuma su kaɗa ƙuri'arsu. In kuma juyin mulki ne irin na soja, wannan tunanin yana nan yana yawo a ƙwaƙwalensu. Wannan ɗan garinsu ne, wannan kuma addininsu guda. Saboda haka sai ya zamana an samu karo a nan. Sannan kuma sai a samu gunaguni ta ɗaya ɓangaren. To me ya sa in mun zama 'yan ƙasa ɗaya, al'umma ɗaya, ba tare da la'akari da bambancin addini da ƙabila ba, me ya sa kowane lokaci Shugaban ƙasa sai dai ya fito daga wani ɓangare na wannan ƙasa, daga ma waɗansu jinsin mutane? Ba a yi adalci ba a nan. Ya kamata ya zama kowanne yana iya yi.

To, in kuma muka ce a ƙyale hannayen adalci su yi aiki da kansu, su fid da mana da Shugaba; kullum hannun adalcin sai su ga kamar yana zalunci ne. Har da tunanin in aka ci gaba a haka za a ci gaba da zama a wani ɓangare ne na zalunci. To, me yiwuwa ma in aka ce, to a shirya kowace ƙabila ta yi; to akwai ƙabiloli ɗari uku da 'yan kai. Za a sha mamaki. Sai dai in kowace rana ɗan wannan ƙabila zai yi shugabanci, sai ya sauka. Shugaban Hausawa ya hau, kashegari ya sauka, wannan ya hau. Ka ga a cikin shekara za a samu shugabanni 364 ke nan da kwata, sannan ƙabilolin ba su ƙare ba. Za a ci da rabon wata ƙabilar, don za su ce su ba su hau ba. Kamar wata ƙabila Kusam, in aka lisafta da su ƙabilolin sun fi ɗari uku a ƙasar. To ya za a yi?

To, kuma idan aka ce tsakanin ɓangarori ne fa, kazalik. Wato an kasa fito mana da fomula guda ɗaya wanda za a ce mana wannan shi ne adala, wanda kowanne zai gamsu da cewa shi ne adalci.

To, sai a zo ga shin, wai mene ne ma adalcin? Shi adalci ɗin nan, wani abu ne da idan mutum ya gamsu da shi sai ya zama adalci, ko ko akwai wani miƙiyasi da za mu iya gane cewa an yi adalci? Don in ba mu san wannan ba, ba za mu iya gane zalunci ba. Da yaya muke fahimtar adalci da zalunci? Alal misali in ka tambayi ɗan Kwaminis mene ne adalci? Koda yake Kwaminisanci ya rushe. Sai su ce maka a ba kowa. Da sukan ce a raba a ba kowa daidai wa daida, tarkacen duniya ke nan, a raba shi daidai wa daida. Sai suka ga ba zai yiwu ba. Sai suka ce a raba daidai gwargwadon buƙata.

To, wajen buƙata ɗin sai aka ce wani yana buƙatar kamar gidan fankacece, har da kududdufin wanka na ƙashin kansa a gidansa. Kuma kamar yana buƙatar motoci kamar guda biyar kuma yana buƙatar gidan shaƙatawa. Wani kuma sai a ce gida mai ɗaki ɗaya ya ishe shi, kuma su uku su haɗu a ɗaki ɗaya, kowa daidai gwargwadon buƙatarsa. Da aka yi wannan, sai mutane suna ganin ga zalunci, amma an ce masa mene? Wai adalci! In ka tambayi ɗan kwaminis mene ne zalunci? Sai ya ce wasu suna da shi, wasu ba su da shi. Shi a wurinsa duk wanda ya mallaki wani abu, to shi azzalumi ne, saboda ya zalunci waɗanda ba su da shi. Wato kamar rigima ce tsakanin waɗanda suke kira ‘have’ da ‘have not’, wato waɗannan suna da, waɗancan ba su da. Waɗancan azzalumai, waɗannan adilai.
Amma duk lokacin da aka samu sauyi, in da waɗannan za su tashi su yayyanke kawunan waɗancan, su kuma sai su zama manya-manyan azzalumai. To, sai ya zama adalci ya kasa ma’ana a nan. Kuma da za ka tambayi Banajariye, mene ne adalci a Nijeriyance? Ina jin shi ma zai yi maka wahalan fassarawa.

To, idan adalci wani abu ne wanda yake da wuyan mu yi masa ma’arifa, to muna iya cewa sai mu komo… ko kuma Allah ya dube ku da fushi gaba ɗayanku. Sau da yawa za ka ga in nau’in zalunci ya zo, ya

zama azzalumi yana yi kuma mutane suna tafe a kai, to za ka ga su ma da kansu gaba ɗayansu sun zama haka nan. Ballantana kuma in ya zama yana zalunci, kuma ana biye da shi a kai, Mabiyansu su ma azzalumai ne. Bahaushe ma yakan ce haka nan. Yarda da zalunci, zalunci ne. In aka zalunce ka, ka yarda a zalunce ka, shi kenan kai ma azzalumi ne, saboda kai ka ba zalunci mafita.

Muna iya cewa, waɗanda suka ba ni wannan maudu'in sun san irin mafitar da zan faɗa. Ba dabara ba ce. Ba cewa za mu yi a tattaro masu ƙwaƙwalenmu a Abuja ba. Babu buƙatar wani abu wai shi 'think-tank' ko 'National Institute for policy and strategic studies', su je su zauna su fidda mana mafita. Mafitarmu wani abu ne wanda Mahaliccinmu ya yi mana. Mu kuma a bisa gaskiya muna da wannan mafitar. Kuma muna iya cewa wallahi, mu da Allah ya yi wa wannan mafitar a birbishin sauran al'umma, muka ɓoye wannan gaskiya da muka sani, to gaskiya babu azzalumai irin mu.

Wani misali da na riƙa bayarwa a wurare daban-daban shi ne, da za a bijiro da mu a ranar ƙiyama, a ce ina musulmin Nijeriya? A ce ma ina Nijeriyawa? 'Yan Nijeriya duk sai su taso. Sai Allah Ta'ala ya ce ina musulmi a cikin ku? Sai su ware. Sai Allah ya ce ku wuce Aljanna, duk gaba ɗaya tunda yake ku musulmi ne. A nan ba a cuci Peter ba, da John da Ciwake da su Taroro da su Nwabuize? Aka ce wai a nan ɗaya muke, ba bambancin addini. Ka ga a nan sai su ce ashe ka san Musulunci shi ne addini na gaskiya, shi ne ko ka ɗan gaya min? Ka ce, da ni da kai duk 'yan ƙasa ne ba bambancin addini? Yanzu ka ga za ka je Aljanna, ni kuwa… A nan ba a cuce shi ba?

To, ashe lallai mu da Allah ya fifita mu da sanasshe mu mafita, sai muka riƙe, muka ce duk cikan mu a zo a nemi mafita, to lallai ba ƙananan azzalumai muke ba. Saboda a rashin yin mu da addini mun zalunci kawukanmu, a rashin yin mu da addini mun zalunci waɗansu, domin ba su ga addinin ba, ballantana su bi. Bilhasali ma sai muka doɗe musu kafar yi, sai muka ce duk ɗaya ne, da mu da ku, ba bambancin addini.

To, ban san ko na yi adalci ga maudu'in nan ba. Ina so ne in yanke maganar da wannan cewa, kullu yaumin ana batun zalunci, na san mutane da yawa za su ce zan taɓo ƙarancin man fetur da yadda manyan ɓarayi suke kwashe kuɗaɗe su kai ƙasashen Turawa, da yadda za ka ji ɗan ƙaramin alhaki Ciyaman na Karamar Hukuma ya wafce Naira miliyan ashirin; amma ni a nawa sai na yi ƙoƙarin na nuna a bisa gaskiya zaluncin duk cikanmu ne.

Na fahimci akwai wani abu guda. Sau da yawa akwai waɗanda in ma ba su yi irin wannan nau'in na zaluncin ba, ba a yaba musu. In kuma suka yi satar ma, ana yabon su a wannan al'ummar. Na san akwai wani da ya samu wani aiki a wata hukuma da ya wafci wasu 'yan kuɗaɗe masu yawa, ya yi hidimomi. Sai aka riƙa yabon sa a unguwa cewa, ka ga yaro da zafin nama. Ka ga Yayansa shekararsa kusan bakwai yana aikin, amma bai samu haka ba. Wannan idan ya daɗe yana aiki irin na Yayansa, me za a gani? Wai ya zama abin yabo, wai yana da zafin nama. Ta nan za ka ga al'ummar gaba ɗaya ita ce azzaluma. Wato gaba ɗaya ne muka taru muka zama azzaluman. Amma kullum muka tashi sai mu ce wani ne ke zaluntar mu.

To, kuma lallai babu shakka, kar mu tsammaci akwai wata mafita gare mu in banda addinin nan. Ina fata, ko ma ban yi adalci ga wannan maudu'i ba; sunan maudu'in zalunci, ni kuma aka ce in yi adalci, wato zan yi wa zalunci adalci. Ina fata daidai gwargwado na ɗan yi. In ma ban yi ba, na tunatar da mu wani ɓangare na zalunci, wanda muke yi wa kawukanmu. Da fatan kowannenmu zai koma gida da tunanin cewa, zai kuɓutar da kansa daga nau'in zaluncin da shi yake a ciki, maimakon ya hango zaluncin wani.

*Wassalamu alaikum warahmatullahi ta'ala wabarakatuhu.*